(١)

## MA’ANAR IBADA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Lallai Allah shi ne Ubangiji na, kuma Ubangijinku, saboda haka ku bauta masa, wannan ita ce hanya madaidaiciya)** [Ali Imran: 51]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai ibada tana da babban matsayi, da muƙami maɗaukaki, ita ce babban manufar da saboda ita ne Allah mai girma da buwaya ya halicci halittunsa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ban halicci mutum da aljani ba sai domin su bauta mini)** [al-Zariyat: 56], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Kafin kai ba mu aiko da wani manzo ba face mun yi masa wahayin cewa lallai babu abin abin bauta wa da gaskiya sai ni, saboda haka ku bauta mini)** [al- Anbiya’u: 25], lallai ibada ne aikin ɗan Adam a dukan rayuwarsa, Imam al- Hassan al- Basriy (Allah ya ƙara masa rahama) yana cewa: lallai Allah bai sanya wa aikin ɗan Adam wani lokaci ba, in ba mutuwa ba.

Duk wanda ya lura da Shari’a Musulunci zai ga cewa: tabbas ibada tana da ma’annoni guda biyu ne; na farko: Gamammiyar ma’ana mai faɗi, ta ƙunshi dukan ƙofofin alhairi, kaman neman arziki, da kyautata ɗabi’u, da gaskiya wajen zance, da yafe wa wanda ya yi kuskure, da gyara tsakanin mutane, da ciyar da iyalai da ɗaukan ɗawainiyarsu, da sauran ayyukan alhairi da

biyayya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(A mafi yawan lokuta babu wani alhairi tattare da mutanen da suke ɓoye maganganun da suke yi a cikin zukatansu, ko waɗanda suke yi tsakanin su da juna; saboda sharri ne ake ɓoye shi, sai dai idan abin da aka ɓoyen ya zamo bayar da umurni ne da yin sadaka, ko aikata wani aiki mai kyau, ko daidaita tsakanin mutane da gyara zumunta, waɗannan kam duka alhairai ne, duk wanda ya aikata haka saboda neman yardar Allah Maɗaukakin Sarki, to kuwa lallai Allah Maɗaukakin Sarki zai ba shi babban sakamako a nan duniya da lahira; saboda abin da ya aikata)** [an-Nisa'i: 114], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: (**Dukan gaɓoɓin jikin mutane suna da nasu sadaka, a kowace ranar duniya: ka daidaita tsakanin mutane biyu sadaka ne, ka kuma taimaki wani akan dabbarsa, ka ɗaura masa kayansa akanta, ko ka sauke kayansa dake kanta sadaka ne, kalma mai daɗi sadaka ce, kowace tako ka yi zuwa sallah sadaka ne, ka kawar da ƙazanta akan hanya sadaka ne).**

Haka ma raya ƙasa ta hanyar noma, da samar da masana'antu, da kyautata ayyuka ta yanda za su amfani ɗaukacin al'umma, hakan kuma ya zama sanadi na cigaba da ɗaukakan ƙasa, duka suna cikin ibadun da Allah mai girma da buwaya yake so, Allah Maɗaukakin Sarki ne ya nemi ɗan Adam da ya aikata haka, a inda yake cewa: **(Shi ne ya farar da halittarku daga ƙasa, ya kuma nemi da ku raya ta)** [Hudu: 61], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai mutumin da Allah Maɗaukakin Sarki ya fi sonsa shi ne wanda ya fi amfanar mutane, kuma mafi alhairin aiki a wurin Allah Maɗaukakin Sarki shi ne: farin cikin da ka shigar a cikin zuciyar Musulmi, ko ka yaye masa damuwa, ko ka biya masa bashin da ake binsa,**

**ko ka kori yunwar da take damunsa, na rantse da Allah, in tafi biya wa ɗan uwana wata buƙata tasa, ya fi alhairi akan in yi i'itikafi a cikin wannan Masallacin –yana nufin Masallacin Madina- na tsawon wata ɗaya.. duk wanda ya tafi tare da ɗan uwansa akan wata buƙata tasa, har buƙatar ta biya, to kuwa lallai Allah zai tabbatar da diga- digansa a ranar da ƙafafuwa suke zamewa).**

Na biyu: keɓaɓɓiyar ma'ana da ake bai wa ibada, inda ta ƙunshi tsayar da ayyukan da suke sha'air ne na Musulunci, da bayar da rukunnansu, irinsu: sallah da zakka da azumi da hajji, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ku mayar da hankali wajen tsayar da dukan salloli, ku kuma dawwama akan haka, ku mayar da hankalinku kan sallarku ta zamo fiyayyiya ta hanyar tsayar da rukunnanta cikin cikakken ikhlasi wa Allah mai girma, ku cika yi wa Allah biyayya da yawaita ambaton sa cikin tsarki da ƙasƙantar da kai wa girman Allah, haka ma ku kiyaye sallah matsakaiciya, wadda ita ce sallar Asubahi, ko sallar La'asar, kamar yadda ijtihadin malamai ya bambanta game da wannan sha'ani)** [al- Baƙra: 238], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, lallai Allah ya wajabta maku yin azumi kaman yanda ya wajabta wa waɗanda suka gabace ku; saboda ku ji tsoron Allah )** [al- Baƙra: **183], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa:** (Ku kiyaye **al'amurran addinin ku, ku tsaida sallah, ku bayar da zakka, duk abin da kuka gabatar wa kawunanku na kyawawan ayyuka da sadaka za ku sami ladansa a wajen Allah, lallai Allah ya san abin da kuke aikatawa, sani irin na wanda yake gani)** [al- Baƙra: **110], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa:** (**Kuma hajjantar wannan ɗaki ya wajaba akan mutanen da suke da iko,**

**duk wanda ya ƙi, ya kuma yi taurin-kai akan umurnin Allah, ya kuma musanta addinin Allah, to, lallai asarar hakan za ta dawo kansa, lallai Allah Mawadaci ne ga barin halittu gaba ɗaya)** [Ali Imran: 97].

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai muna ƙara tabbatar da cewa: cikakken mutum shi ne wanda yake da daidaito wajen gabatar da ayyukan da Allah Maɗaukakin Sarki ya farlanta na sallah da azumi da zakka da hajjin farali ga wanda yake da iko, da kuma raya doron ƙasa, da riƙo, da kuma yin ado da kyawawan ɗabi'u.

Haka ma muna ƙara tabbatar da cewa ita ibada da keɓaɓɓiyar ma'anarta ba ta isa zuwa ga manufa sai idan ta yi tasiri a cikin ɗabi'un mutum da tsarin rayuwarsa, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa:**(Lallai sallah tana hana aikata alfasha da abubuwan ƙi)** [al- Ankabut: 45], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Idan ranar azuminku ya yi, kada ku yi zance batsa, kada kuma ku yi faɗa- faɗa, idan wani ya zage ku, ko ya neme ku da faɗa, to ku ce: mu muna azumi..)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai an aiko ni ne saboda in cika kyawawan ɗabi'u)**, duk wanda ya ɗara ka a fagen ɗabi'u masu kyau, to lallai ya ɗara ka a fagen fahimtar ingantaccen addini.

**Ya Allah Ubangiji ka taimake mu wajen ambatonka da gode maka da kuma kyautata yi maka ibada.**